Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "Eulogy for Ahmad Tijani." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-0695-yabo-ga-ahmad-tijani/.

# Yabo ga Ahmad Tijani

[Page 1]

Alḥamdu lahu wa lā ilāha ghayruhu

Mun bi Sarki wanda Ya yi mu

Wanda yayyo shugabanmu

Shi ka ceto ran Qiyāma

Annabinmu Muḥammadun fakewa

Bayan Bismillah Allah

Mun Ṣalāti gun sa Allah

Wa sahabbai nai don Ḥawāluh

Har ɗiya nasu duk muke gamawa

Yan uwa ku taho Mujālah

Mu yi gudu don sonsa Jallah

Mu yi riƙo wurudi da Ṣallah

Lāzimi daɗa shi muke gwadawa

Kaito wawa ba shi dubi

Ga fa hanya babu ruɗi

Babu yunwa sai fa jiɓi

Ba ƙishirwa, babu kwarin ɓacewa

Kaito kaito da kai guba

Ka ƙi bin labin Waliyyi

Ga shi ko jikan nabiyyi

Shehu Ahmadu ne abin yabawa

Shugaban waliyyan zamani

Nasu har nau gunsa zan yi

In yabe shi in ce "Tijani

Kama hannuna daren tsayawa"

Shi ka ba ceto Qiyāmā

Ka fatan zamaninsa su ma

An daɗa bisa ba nadama

Shekara ashirin akan daɗawa